# Surah 99: Al-Zalzalah - سورة الزلزلة

بسم الله الرحمن الرحيم

[99:0] Bismi ***ALLAH***, Alrahman, Alrahim.*

إِذَا زُلْزِلَتِ ٱلْأَرْضُ زِلْزَالَهَا ١

[99:1] Idan aka girgiza qasa, girgiza mai tsanani.

وَأَخْرَجَتِ ٱلْأَرْضُ أَثْقَالَهَا ٢

[99:2] Kuma qasa ta fitar da kayanta, masu nauyi.

وَقَالَ ٱلْإِنسَٰنُ مَا لَهَا ٣

[99:3] Mutum zai yi mamaki: "Me ke faruwa ne?"

يَوْمَئِذٍ تُحَدِّثُ أَخْبَارَهَا ٤

[99:4] A ranar nan, za ta ba da labarinta.

بِأَنَّ رَبَّكَ أَوْحَىٰ لَهَا ٥

[99:5] cewa Ubangijinka Ya yi umurni zuwa gare ta.

يَوْمَئِذٍ يَصْدُرُ ٱلنَّاسُ أَشْتَاتًا لِّيُرَوْا۟ أَعْمَٰلَهُمْ ٦

[99:6] A ranar nan, mutane za su fito dabam-dabam daga ko'ina, domin a nuna masu ayyukansu.

فَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ خَيْرًا يَرَهُۥ ٧

[99:7] Duk wanda ya aikata aikin alheri na misqala zarratain, zai gan shi.

وَمَن يَعْمَلْ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ شَرًّا يَرَهُۥ ٨

[99:8] Kuma wanda ya aikata aikin sharri na misqala zarratin zai gan shi.